HIRA DA ALHASSAN ALHASSAN UBAN XAKIN ZARUMAWA, HAKIMIN KUYALLO

Tambaya: Ranka ya daxe ya sunanka?

Amsa: Sunana Alhassan Alhassan Uban Xakin Zarumawa, Hakimin Kuyallo.

Tambaya: Muna so ne mu sami bayani a kan waxannan rikice-rikice da ke faruwa a wannan vangare naka, dangane da asalin tarihin abin, da kuma tsananin abin.

Amsa: Wannan al'amari ya shafi kusan duk qasar Birnin Gwari, amma ya fi tsanani ne a wasu gundumomi kamar guda huxu ko biyar, amma sauran ma ba babu su ba ne, da ake magana a kan gundumata ko kuma tarihin abin tun farkon shi ya xauko tarihi ne tun alif da xari tara da tasa'in da takwas (1998) lokacin da wasu gungun Fulani suka zo wata gudummuwa da ake kira Kuyallo inda yanzu nan nake, har suka kashe mutane da sauransu. Daga nan kuma suna ci gaba jefi-jefi har a lokacin da farar hula ta karvi mulki, abin sai qara tsananta yake yi.

Tambaya: To wannan zuwan nasu na farko wane abu ne ya jawo rigimar?

Amsa: A wancan lokaci a zaman makiyaya suka zo, ko da yake ba mu san inda suka samoi shanun ba, to sai suka samu savani da mutane har suka kashe mutane a wurin.

Tambaya: Ranka ya daxe daga ina suka zo, ainihin daga cikin masarautar Birnin Gwari ne ko kuwa?

Amsa: Ba masarautar Birnin Gwari ba ce domin a lokacin ba wanda ya san daga inda suka fito, an dai gansu sun shigo suka shiga gonakin mutane suna varna a wannan lokacin.

Tambaya: Kuma an gane su ko mutanen ina ne ko daga ina suka zo ko an san su?

Amsa: Babu wani abubuwa da za su nuna an san su, domin sun zo ne ba ma da siffar ko varayi ko 'yan fashi ba, ko wani abu ba, domin mu mun xauka kamar makiyaya ne suka zo don su samu savani da manoma, a wannan lokacin shigar da suka yi ke nan amma ba wanda zai ce ga inda suka fito tun da a wannan lokacin ba a

zama (serious) ba, ba a damu da in an ga wani abu a yi sauri a yi maganinshi ba. To, da aka yi wannan aka wuce sai jefi-jefi abubuwa suka zo har aka kai ga sace-sacen shanu, to kamar yadda wannan a taqaice haka yake ta satar shanun nan da aka fara da za a zo da motoci ne a yanka shanu a sa a cikin mota a wuce har ta kai ga za a zo a riqa xaukar shanun manoma waxanda ake tura wa, wato masu huxa ke nan waxanda ake sa wa garma, abu har ya kai ga sun kwashe shanun manoma Hausawa ke nan, ta kai ga suna bin ruga-ruga suna kwashe shanu, ta kai ga har ma suka kashe masu shanun.

Tambaya: Su kashe mutane syu kore su su kwashe shanun ke nan?

Amsa: Eh! Duk wanda ya kawo turjiya za a kore shanunsa sannan su kashe shi, har ta kai ga suna kwashe shanu sannan su yi fasiqanci da mata. Har ta kai ga gonakinmu da ke kusa da iyaka da dazuzzuka ba ma iya nomawa dmomin idan suka tafi gona ko dai a sace ko a kashe su ko kuma a yi masu duka a qwace abin da suke da shi.

Tambaya: To ya nuna ke nan a dazuzzukan nan suke ba zuwa suke yi ba?

Amsa: E to, kamar ni a yankina muna da babban dajin da muka yi iyaka da Zamfara, to mu a nan ba su a cikin wannan dajin da muke ciki amma suna cikin wannan dajin na Zamfara, saboda za su zo cikin gari su yi ta’asa sannan su koma cikin wannan daji

Tambaya: Ranka ya daxe akwai wasu wurare da aka keve domin Fulani su riqa yin kiyo suna ciyar da shanunsu inda ba gonaki bane, kamar yadda ake cewa....

Amsa: Wato a da lokacin da ake zaune lafiya, gwamnatin Jihar Kaduna ta keve wani daji wanda ake ce mashi wato (Grassland reserve), babu shakka akwai amma Fulanin da ke qasar Birnin Gwari sun fi qarfin irin wannan (Green Grasland reserve) xin. Domin a duk gungumomin nan babu inda za ka je ba ka samu sama da setlement na Fulani ba, ban da ma masu zuwa su wuce saboda akwai qasa akwai dausayi akwai komai. Saboda haka, wannan

Green reseerve) xin ma ba zai xauke su ba, kodayake akwai wasu suna cikin Green reserve xin.

Tambaya: Ranka ya daxe shin wannan reserve xin tun na farko wanda aka samar shi ne har yanzu ko an maida wasu gonaki ne ko kuwa yawan makiyayan ne ya qaru har ya sa ba zai gamsar da su ba.

Amsa: A'a, ba a mai da su gonaki ba, sannan a inda suke mai martaba ya sa an kare su babu wanda ke da ikon ya shiga ko ya yi wani abu a wannan wurin. Har ila yau hakimai irina sun sa an yi daba daba a iyakokin wuraren ta yadda babu mai iko ya shiga.

Tambaya: Ranka ya daxe wani abu da yake xauke kai shi ne cewa masu shanu na wa manoma da ke xaure da shanun a gida, akwai lokacin da sukan zo su kore shanun duka su tafi da su.

Amsa: Wannan haka yake ba ma na manoma kaxai ba, har na kiwo da duk wasu shanu da ka sani za su zo da adda da wuqaqe su sassare igiyoyin da aka xaure shanun ko kuma su ce ka kwance da kanka in sun ganka.

Tambaya: Ranka ya daxe wane yare suke yi?

Amsa: gaskiya mafi yawancinsu in sun zo suna yin Hausa ne amma ana kyautata zaton Fulani ne.

Tambaya: Amma ranka ya daxe ya dangantakar manoma da makiyaya a wancan lokacin kafin zuwan wannan matsalar?

Amsa: Mu ba mu tava samun wata matsala na tashin hankali tsakanin Fulani da manoma ba, sai dai na al'ada wanda aka saba samu wanda ake zuwa wajen mai unguwa ko kuma in ta yi tsanani ne sai a je wajen 'yan sanda a kimanta abin da aka yi na varna a biya shi ke nan. Sai da waxannan varayi 'yan fashi masu fyaxe suka zo suka fara waxannan abubuwa.

Tambaya: Akwai wani qarin bayani da za ka yi mana ne?

Amsa: A'a, in dai tun da akwai 'yan uwana hakimai, za su yi maku bayanai, sai dai qarin bayanin da zan yi a kan gwamnatin jihar Kaduna da ta tarayya, akwai lokacin da suka turo (force) wato sojoji da 'yan sanda suna shiga wuraren amma abin ka da gwamnati da ba'a tambayan me ya faru mutanen nan sun samu

resistance sun samu imunity sai su sake dawowa saboda ‘yan sandan sun zo sun wuce wani lokaci har gayyata ta suke yi.

Tambaya: Amma ranka ya daxe tambayar da nake son yi, ainihin Fulani waxanda ake tare da su ya dangantakarsu take da waxannan ko in sun zo suna haxewa ne na waxancan.

Amsa: Eh! Wannan wata tamya ce wadda za a iya cewa da wuya a ba da amsa domin mu dai mun san a wancan lokacin Fulani da muke tare da su lafiyayyu ne, amma lokacin da abu ya gurvata, to baka iya shaidar su domin duk Fulani Fulani ne. domin yadda ake cewa ma za su zo rigarka in sun san kana da ‘ya’ya za su ce to ko mu kashe ka ko ka ba mu xanka xaya amma wannan wani jita-jita ne.

Tambaya: Ke nan wannan yaron da ka ba da za a je da shi a ci gaba da irin wannan aiki da shi ne?

Amsa: Eh, ba shakka ai wai ka ba da gudummuwarka ne ai kamar za a yaqi ne sai a ce ka kawo gudummuwarka wai su a wurinsu ke nan.

Tambaya: To kamar idan manomi ya ba da xansa?

Amsa: A’a, ba manomi ba, Fulani dai yaron Fulani tare da su na ainihi ke nan. Domin su yaqi qila manoman ke nan.

Amsa: Su yaqi ‘yan uwansu ma ba manoma kaxai ba.

Tambaya: Amma ranka ya daxe me ya sa kake ganin suke yin irin waxannan ko kana ganin babu wani dalili?

Amsa: Eh akwai dalilai da yawa. Na farko ni a nawa ra’ayin qungiyar miyatti Allah ta qara contributing domin akwai lokacin da ta xaure wa Fulanin gindi suna abin da suka ga dama, ta kuma zo ta cutar da Fulanin ta koma ta wurin ‘yansanda abin da nake nufi a nan shi ne, idan rigima ta haxa ko da Bafulatani ne da Bahaushe ko bafulatani zai laifi sai a kai wajen ‘yansanda, su qungiya suna da Agent xin su a wurin ‘yansanda sai a zo a cutar da Fulani ‘yan uwansu su koma su haxu da ‘yan sanda su yi cuwa-cuwarsu. A wancan lokaci ni na san hakan. Daga nan yaran Fulani sai suka vaci. Da akwai wani abu da ake kira “Kurga” ko? Sai a tura yaro,

wato wancan na xaya ke nan, wato dangantakar Fulani da ‘yansanda da qungiyar Miyatti Allah ba ta da kyau a wancan lokaci, ko kaxan. Don mu mun gani a nan ka san birnin Gwari. To sai kuma Kwargo da aka riqa yi, ka ga an saki xan yaro xan shekara 18/25 da shanu fiye da xari ya tafi ya yi ta bushasharsa, idan ma ya ga wani san ma ya kora cikin nashi iyayen na gida ba ruwansu. Da kuwa saninmu Bafulatani ne zai zo da iyalinshi da jakuna da komai da komai har ma mutane su riqa Allah-Allah ya zo su ba shi wurin sauka, yanzu kuwa wannan sai ya kau, sai a ba xan yaro ya tafi ya yi varnarsa. Wannan sun yi contributing.

Tambaya: Ranka ya daxe, mene ne ku shuwagabannin al’ummomi kuke yi domin ku ga an magance su?

Amsa: Eh to, babban abin da muke yi kamar yadda muke yi da ku yanzun nan a duk sati muna kaiwa mai martaba rahoton abin da ke faruwa. Sannan kuma da mun san da zuwanku da mun shirya qila da mun qara haxa maku wasu data/informationta shanun da ake sacewa da sauransu. Mu iyaka gudummuwarmu ke nan tun da bamu da ‘yan sanda ba mu da iko da soja, ba mu da kowa sai dai mukan yi mobalizing yaranmu suna kewaya gari har da daddare.

Tambaya: ‘Yan bajilanti ke nan?

Amsa: Eh, to muna iya kiran shi bijilanti ko mu kirasu ‘yan sa kai, domin bijilanti suna da wani qungiya. Domin idan aka ce ga xan bajilanti sai ma su iya kashe shi, su miyagun duk inda aka ce ga xan banga ba wanda suka qi jini irin xan banga, domin daman mun yi amfani da su ‘yan bangan mun ci nasarori to sai suka zo suka sake farauta.

Tambaya: To, yanzu ana nufin cewa suna da mutanen da suke kai masu labari ke nan?

Amsa: Wannan zai iya yiwuwa, domin in babu su ai ba za su oya cin nasarar abuuwansu ba, duk wanda zai yi aiki ai sai ya shirya yanda zai yi aikin.

Tambaya: Ranka ya daxe da wane lokaci ne suke yin aikin, ma’ana lokacin da suka fi zuwa da damina ne ko da rani ko ko?

Amsa: Kullum ko wane lokaci suna zuwa babu lokacin da ba su zuwa.

Tambaya: Kuma waxanne lokuta suka fi kawo hari?

Amsa: Kowane lokaci, da safe ko da rana ko yaushe. Yanzu haka bacin da Allah ya sa gwamna ya sa sojoji da ‘yan sanda suna patrol ko da yaushe a kan hanyar nan to wallahi ba ka isa ka biyo ba kan wannan titin Birnin Gwari zuwa Funtua ba, sai ‘yan fashi sun tare ka.

Tambaya: To yallavai nan inda kake wakilta, ko masarautarta

Amsa: A’a, masarautata dai ko inda nake wakilta ko gundumata? Hahaha

Tambaya: To inda kake wakilta ko kake hakimci kana sa ran akwai hasaran rai ko na dukiya?

Amsa: To wallahi in banda xan tsakanin nan babu ranar da asarar rai ba ma dukiya ba, domin a hanyar nan babu ranar da ba za a yi fashi a kashe mutum ba, babu (average of one person) a qalla ko wace rana ni na tabbatar da hakan, abin ba kyau.

Tambaya: Ranka ya daxe gwamnati me take yi domin magance wannan abu don muna ji a kafafen yaxa labarai da gidajen radiyo da sauransu cewa an magance kusan kashi tamanin 80% na matsalolin makiyaya da manoma a wannan....

Amsa: Eh ba shakka wannan sabuwar gwamnatin lokacin da take yin kamfen ta yi alqawura da dama, har da cewa ba shakka za ta san yadda za ta yi da miyagun nan kuma alhamdulillahi da suka hau sun yi abin da za su yi. Mai martaba Sarkin Birnin Gwari ya tuna wa gwamna kuma gwamnati ta turo security agent an shiga dajin an yi abubuwa da sojoji da ‘yan sanda da sauransu. Wannan shi ya sa aka xan ji sauqi kaxan amma har yanzu suna nan cikin dajin nan suna abin da suka ga dama. Kuma the worst shi ne satan mutane da ake yi don da sun qare satan mana shanu shi ke nan sai su zo su kama mutum da wayarshi, sai su tafi da shi daji a bugo waya ga wane ga kuxin da za ku bva mu a sako shi,

ta kai ga ma akwai sanda suka ce ga kuxin da za a ba su aka ba su kuxin kuma su kashe mutumin. Ta kai ga kuma sukan ce a ba su kuxin aka ba su suka kashe waxanda suka kai kuxin, kuma suka kashe wanda suka kama. To yanzu aikin da ya fi tsanani su ne mutane su ne shanun kuma.

Tambaya: To wai akwai wasu irin mutane da suke kamawa ne kokuwa kowa suke kamawa.

Amsa: To, ai ya kamata in bari saura su amsa kada in wuce gona da iri.

Tambaya: Ranka ya daxe, Allah ya ja zamaninka, sunan ranka ya daxe.

Amsa: Ibrahim Abdullahi Magajin rafin Birnin gwari, Hakimin Kazage.

Tambaya: Kamar yadda muka fara muna tambaya ne a kan wato ita wannan masarautar taka, muna so mu ji tarihinta da kuma wato yadda ya zama wato abin damuwa ga mutane.

Amsa: Ah ai wannan magana ka ganmu nan hakiman nan kowa ta shafe shi, amma kusan in ce mu huxun nan ba irin mu, kusam ma ni in ce ba iri na, kamar mu biyun nan ni da xan Darman mu muke da daji wanda yake varayin nan suna nan a ciki damfare, wanda yake in sun je sun yi ta'asan nan gurun su dai su shiga dajin yanzu haka, ba ka iayakance bahillacen da ke cikin dajin, yanzu matsalar ma da ta fi damunmu shi ne qauyukan da ke kusa sun koro mutanen masararsu da suka shuka ita suke ci sun ce duk shegen da ya koma qauyen sai sun kashe shi. Sun kori mutanen sun mayar da qauyen nasu. Mun rubuto mun kaiwa sarki a kan wannan al'amari. Kuma satar mutanen kusan ni yanzu a qasata kusan mutum goma sha biyu 912) ke nan aka sato wanda yake an kashe mutum huxu (4) an biya kuxi an sako sauran.

Tambaya: A cikin waxanda aka saa?

Amsa: Eh, a cikin waxanda aka sata an kashe mutum huxu, kuma matsalar yanzu qauyen gonakin da aka bari ba a noma ba suna da yawa, saboda suna nan a cikin dajin dabbobinsu na nan kuma qauyen bai shigo.

Tambaya: To sun gina gidaje ne a wajen ko yaya?

Amsa: A’a, gidaje suka kori mutanen nan suke ciki, kuma ba su da wani gida tun da suna tsoro in sun kwana nan gobe sai su tashi su koma nan.

Tambaya: Sai su tattara shanun su koma wani wuri ke nan?

Amsa: Eh, haka ne, amma maganar satar shanu kullum ne ko jiya, n zo gidanka da bindiga a kore ka a kore shanun ko jiya.

Tambaya: Amma gidan da suke zuwa su kore shanun gidan na su wane ne, na Fulani ne ko kuwa?

Amsa: Eh na Fulanin ne ai Hausawa ba shanun yanzu, wani bafullatanin an sace

Dan shi an sace shanunshi shekaran jiya, suka zo suka sake kore matan xan kuma duk Fulani ne ‘yan uwansu.

Tambaya: Toh, yallavai kamar su waxannan Fulanin da ake zuwa a yi masu ta’asan zaunannu ne ko suna da alaqa da waxancan?

Amsa: A’a, ko kaxan su zaunannu ne kuma ba su da alaqa da waxancen saboda ba wanda bai shekara ashirin ko talatin (20-30) a zaune a garin ba, kuma mafi yawancin Fulanin namu ai duk sun kore su sun tashi, sai xaixaiku ne waxanda suka yi shahada suke zaune su ma kuma an zo ana ta kore shanunsu.

Tambaya: To, wannan in sun kore shanun nan ina suke kai su?

Amsa: cikin dajin suke kai su8.

Tambaya: To me suke da su?

Amsa: To waya sani? Sanin gaibu sai Allah.

Tambaya: Ba’a da wani masaniya na inda suke zuba wasu sai ko..

Amsa: To Wallahi mu dai ba mu iya bada shaidar wannan. In dai an sace can suke zuwa da su daji kuma dai bai shigo.

Tambaya: Ba a da labarin a wata kasuwa ko?

Amsa: Akwai kasuwanni amma dai ko ka je ba za ka gani ba, kasuwanmu bai wuce Sabuwa, Sabin Birni da sauransu ba. amma wani lokaci wasu sun ce akan samu, amma ni dai ba sani ba. amma labari na zuwa wani lokaci an ce sukan vullo hanyar legas su tare mota su zuba su wuce da su.

Tambaya: Ok! Ana samun wannan labarin?

Amsa: Eh! Ana samun wannan labarin. Don akwai wani wuri ana ce mashi mai Daro, da nan suke loda shanun suna nufar kaduna da su, to sai wata ran sai sojoji suka kama su, daga nan sai suka xage qafa sai suka sake hanya. Yanzu ba mu san inda suke zuwa ba.

Tambaya: Ya kake ganin wannan fitinar da tattalin arziqi na wannan yanki naku?

Amsa: To, ai mu an kashe mu wallahi an kashe mu wallahi, ni na san Bafullacen da bai gaza mallakar sa xari biyar ba, kuma ya zo qasannan bai da shanun da suka kai bakwai, nan Allah zai mashi arziqin yai noma ya tara shanun, amma yanzu wallahi bai da zakara xaya wallahi duk wannan abin ya kashe kusan gaba xaya.

Tambaya: A gundumarka akwai irin kamar su zo su qone gida ko makamancin haka?

Amsa: A'a, ba mu samu wannan ba

Tambaya: Sai dai su zo su kashe mutane su ...

Amsa: Sai dai su shigo qauyuka su kashe mutane ko kore shanu.

Tambaya: Suna yin fasiqanci ko kuwa?

Amsa: Eh! Suna yin fasiqanci sosai

Tambaya: Sukan saci 'yan mata ne ko kuwa?

Amsa: Eh! Sun saci 'yan mata, yana nan a report xin mu sun saci 'yan mata ko uku ne sun dawo da su. Akwai kuma mutanen da gaba xaya Zamfarawa su gida ya fi ashirin sun kore shanun, daga baya kuma suka dawo da matan da suka xauka, suka zo suka tattara kayansu, haka suka zo na basu takarda suka tashi saboda fasiqanci da matan da varayin ke masu.

Tambaya: To ran ga ya daxe ko da yake ba wani abu ba ne wanda qila za ka iya sani, amma yanda suke kamar samun abinci da sauransu?

Amsa: To Allah kawai ya sani.

Tambaya: Ba sa xiba in sun kawo hari?

Amsa: A'a, ba su xiban abinci, yanzu ne dai suke mana tsiya mutanen da suka kora in masararsu ta yi ita suke karyewa suna ci yanzu fa

halin dsa ake ciki ke nan don na san agwan da ko taki ya sayi ya fi buhu xari amma yanzu ko abin naira bai samu a gonarsa ba.

Tambaya: Bai ma iya zuwa wurin ke nan?

Amsa: Bai ma iya zuwa wurin masarar ta yi sun karye masarar sun cinye. Shekaran jiya ya zo.

Tambaya; Ya sunansa?

Amsa: Sunanshi Hassan

Tambaya: Na ce bayanin da ka yi na waxannan zamfarawa da aka sace shanunsu kuma aka zo ana satar matansu yara ne ko kuwa?

Amsa; Eh yara ne ake sacewa, sun tashi ma sun bar wajen sun bar qasar ma wallahi.

Tambaya: So waxanda ake xauka ‘yan mata ne da za a iya fasiqanci da su.

Amsa: Eh wallahi, kwana xaya kawai suke yi da su sai su dawo da su ko biyu. Akwain ranar da suka zo suka tara mazan a gefe kan idonsu aka yi fasiqanci da matan. Bayan da za su yi saboda ga wasu a tsaye da bindigogi, to daga ranar ne washegari suka bar qasar gaba xaya, wato ranka ya daxe ka ga idan ka fito Kaduna daga Iyafot idan ka baro iyafot wannan dajin na rantse da Allah wannan dajin ba komai ciki sai varayi.

Tambaya; wato a cikin dajin?

Amsa: Eh a cikin dajin, su ne suna nan ka ga daga Maganda Saulawa zuwa tsohon garin Gwari dauji ne daga nan ba gida har sai ka haxa da iyafot saboda iyayenmu sun bi da mu da qafa ko ina. Ni yanzu idan ka ce ka raba ni da gari kilomita biyu da qafa to ba zan je ba, saboda in zan je birnin Gwari yanzu idan na shigo mota yau gobe ba ita zan shigo ba tun da mu yanzu hakonwa suke dukkanmu nan muna cikin haxari tun da duk hakunmu suke, ka gan shi nan wannan an sace dakacin shi an kashe, shi nioma an sace dakaci na an kashe shi.

Tambaya: a gida suke zuwa su kashe su?

Amsa; Eh! A gida suke zuwa da daddare suka buxe wuta suka kashe shi.

Tambaya: To a qafa suke zu7wa ko a babura?

Amsa: Eh a babura suke zuwa, abin da ba tsoro suke ba, ga bindiga ba dole mutum ya kauce ba.

Tambaya: To amma Gwamnatin akwai wani abin da take yi ko na harkar jami’an tsaro ne?

Amsa; Ah, yanzu ni ai akwai sojoji a Damarin. Allah ya taimake mu da gwamna ya zo aka yi camp na sojoji ai da mun bani saboda suna tsoron sojojin yanzu garin bai shiguwa amma qauyuka ko sun fa kore qauyuka

Tambaya: Ok qauyuka waxanda suke da qananan population su ne aka kore su ba mutane?

Amsa: Eh sun hana su zaman qauyen sun dawo cikin gari munanan tsambare da mu da su a cikin gari.

Tambaya: A cikin gundumarta akwai waxanda suka fita gudun hijira?

Amsa: Zuwa wani qasar?

Tambaya: Eh

Amsa: A cikin qasata suke gudun hijira na qauye ne suke shigowa cikin gari da yawa suna nan sun kai xari biyar.

Tambaya: Ba a noma ba komai?

Amsa: Ko na qasan wannan da suka gudu sun kai xari uku suna nan qasana

Tambaya: Subhanallahi, ranka ya daxe muna godiya

Amsa: Da saurana ina zuwa, akwai wani gari qasar wannan ne so fa gaba xaya garin Dakaci ne da masu unguwanni yanzu garin ba kowa sun kori kowa sai su kaxai a garin. To daga nan ni na gama magana, hanyarmu qarfe 5 ba ta yi kana hanya.